Haramta giya ya sauka ne kuma ana yin ta daga abubuwa biyar ne: inibi, dabino, zuma, alkama, da sha'ir"

Daga Abdullah Dan Umar -Allah ya yarda da su- cewa Umar ya ce:- yana kan minbarin Manzon Allah tsira da aminci su tabbata a gare shi:" Bayan haka, ya ku mutane,tabbas hukuncin haramta giya ya sauka alhaliana yin ta ce daga abubuwa biyar: Inibi,da Zuma,da Alkama da Sha'ir; bin da ake cewa giya: Shi ne duk abin da zai gusar da hankali

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim suka Rawaito shi]

Umar Dan Khaddab -Allah ya yarda da shi- ya yi huduba a masallaci Manzon Allah -tsira da aminci su tabbata a gare shi- kuma akan minbarinsa, kuma ya tabbatar da cewa lallai giya itaa ce duk wani abu da zai iya jirkita hankali, ba wacce aka yi da inibi ba kawai, duk wani abin sha wanda zai iyi jirkita hankali ko da kuwa da dabino ko zuma ko alkama to suma sun zama giya, kuma hakika Uma r ya fadi abubuwa uku a cikin Hududbarsa wanda akawai rikitarwa a cikinsa kuma yayi burin ace Annabi yana raye, cikim wadan nan abubuwa guda uka da ya da aka kure matuka izuwa gare shi sune Gadon Kaka, da Gadon Mamacin da bashi da Da ko Mahaifi, da wasu abubuwa kan Riba, kuma Alhamdulillah cewa lallai Hukuncin wannan abubuwa guda uku sananne ne, kuma wannan ba yana nufin cewa Annabi baiyi bayaninsu ba Hakika Annabi ya Isar da Sakonsa, kuma ya bada Amana, kuma ya isar da sakon Allah abun da yafi wannan ma buya da kuma wanda ya fi wannan ma girma kuma Umar yana son yakasance akawai nassi gwari gwari ne a kansu da baya bukatar wani Ijtihadi.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/2954